





An yi wani zaki sarkin dawa.

Zaki ya kore ƙananan dabbobi daga dawa.




Ya ce ba ya sarautar ƙananan dabbobi.



Sarki ya kori kunkuru da zomo.

Ya kori tsuntsu da biri.

Ya kuma kori zakara da ɓera.


A cikin dawan sarki sai
manyan dabbobi.
A dawa akwai giwa da
doki.
Akwai koma jakin-dawa da
damisa



Wata rana zaki ya faɗa




cikin raga.

Dabbobin dawa sun ji

kukan zaki.

Dukansu sun fito su taya




sarki.

Giwa ta ja raga da hanci.

Doki ya taka raga da ƙafafonsa.

Zaki bai samu tsira ba.







Dukan manyan dabbobin

dawa sun kasa.


Jakin-dawa ya ce a nemi

ɓera.

Sarki ya ce ɓera ba ya dawansa.

Jakin-dawa ya ce sai a nemo ɓera.



Jakin-dawa ya sami ɓera.

Ɓera ya tsinka raga da

haƙoransa.

Zaki ya sami tsira.